# NI MUSULMI NE

NA

MUHAMMAD ASHRAF SALAH

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَنِ الرَّحِيمِ

DA SUNAN ALLAH MAI YAWAN RAHAMA MAI MATU{AR JIN {AI

﴿ وَمَن يَبْتَغِ غَيْرَ ٱلْإِسْلَٰمِ دِينًا فَلَن يُقْبَلَ مِنْهُ وَهُوَ فِي ٱلْأَٰخِرَةِ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ ﴾ [آل عمران : ٨٥]

*85.* Kuma wanda ya nẽmi wanin Musulunci ya zama addini, to, bã zã a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a Lãhira yanã daga cikin mãsu hasãra.



**Copyright, distribution and translation are reserved for every Muslim**



| | |
|---|---|
| **Legal Deposit No.** | **22274 / 2008** |
| **International Serial** | **977-6157-64-5** |

**For charitable distribution call:**
**0020101459613**

**For suggestions e-mail:**
**anamuslim@windowslive.com**

**WWW.Iam-Muslim.com**

# IMANI DA ALLAH

**Ni Musulmi ne…….**

**·Na yi imani da Allah shi kaxai, ba shi da abokin tarayya, babu wani ubangiji bayan shi, bai haifa ba, ba a haife shi ba, sam ba shi da kwatankwaci.**

**·Mahaliccin sammai da qassai, kuma mamallakinsu, masanin abin da ya vuya da abin da yake a bayyane, raya-yyen da ba ya mutuwa, tsayayyen da ba ya barci.**

**·Yana da sunaye kyawawa da sifofi maxaukaka, a cikinsu akwai sunaye casa'in da tara, wanda ya kiyaye su ya**





**kuma roqi Allah da su ya shiga aljanna.**

**·A cikinsu akwai sifofin kaxaita Allah, shi mai girma da xaukaka shi ne "al-waahidu" al-ahadu" "al-fardu' (ma'ana shi xaya ne tilo), shi ne ake nufi da buqata, mamallakin kowa da komai kuma mai mulki.**

**·Da sifofin xaukaka; ka ga shi ne mai yawan hikima, qwararre, mai shirya-tarwa, kuma shi ne gaskiya, na farko da na qarshe, na bayyane da na voye, wanda zai gaje komai kuma wanzajje, mawadaci kuma mai tsarki, mahalarci makusanci, mai hukunci mai adalci,**

hasken sammai da qassai, ma'abocin xaukaka da karamci.

·Da sifofin girma; shi ne mabuwayi mai xaukaka da girma, mai sa a yi dole, mai tsananin qarfi, wanda ya rinjayi kowa, mai iko kuma mai qaddarawa, mai taimako maxaukakin da babu irinsa.

·Da sifofin iko; shi ne masani mai ji mai gani, rayayye.







mai riqewa mai shimfixawa, mai dankwafarwa mai xaukakawa, mai buwayarwa mai qasqantarwa, mai bayarwa mai hanawa, mai amfanarwa mai cutarwa, mai rayarwa mai matarwa, mai qaddamarwa mai jinkirtarwa.

·Da sifofin da suke nuna halittunsa; shi mahalicci ne mai yin abu ba da misali ba, mai surantawa mai samar da komai, gwani wajen qirqirar halitta ba tare da ya ga ta wani ba, mai dawo da abu mai tashin komai, mai tattara komai mai yawan baiwa da yawan buxi, mai yawan azurtawa mai wadatarwa, wanda ya san qididdigar komai, shi ne wanda ya mamaye komai, mai

kiyayewa mai lura da komai, mahaliccin sammai da qassai.

·Da sifofin rahama; shi ne mai rahama mai jin qai, mai tausayi mai baiwa, mai son bayi mai kyautatawa, mai kuma yawan gafara da afuwa mai amsar tuba, mai aminci da bayar da kariya da tsaro, mai tausayi, wanda ake gode masa, mai karamci da ni'imtarwa, mai baiwa mai taimako, mai amsar addu'a mai yalwa mai haquri mai shiryatarwa, mai yawan haquri mai yawan tausasawa, majivincin al'amurra, mai ceto mai taimako, mai karvar tuba.

·Ya yi wa xan adam ni'imomin da ba su da iyaka, babu wata ni'ima da bawa yake ciki face daga Allah shi kaxai take, shi ne wanda ya halicce shi ya kuma raya shi, ya kuma sanya masa ji







da gani, ya karrama shi ya kuma kyautata masa.

·Saboda haka ne ya zama wajibi akan bawa ya kaxaita Allah shi kaxai wajen bauta –wadda ita ce aikata abin da aka bayar da umurni da nesantar abin da aka hana-, domin babu wani da ya cancanci ibada sai Allah.

·Haka ma lallai Allah ya san dukkan halayen da bawa yake ciki, shin na xa'a ne ko na savo, dole ne bawa ya cika zuci-yarsa da ganin kwarjinin Allah mai tsarki da xaukaka, da ganin girmansa da sonsa, ya kuma ji kunyar sava masa, ya nesanci haka saboda Allah yana ganinsa, ya kuma san abin da yake yi na savo.

·Ya yi farin ciki da kyawawan ayyukan

da zasu kusanta shi da yardar mahaliccinsa mai girma da xaukaka, ya kuma ci gaba da aikata su har ya sami matsayin "al-ihsan"; saboda imani yana qaruwa da qaruwar xa'a, yana kuma raguwa da aikata savo.

·Ka da ya miqa ragamarsa ga sha'awa ko son zuciya ko bidi'a, ya miqa ragamarsa ne kawai ga Allah shi kaxai, yana mai bin umurnin Annabi (sallallahu alaihi wa sallam), ka da manufarsa ta aiki ta zamo neman karikitan duniya, a maimakon haka ya nemi ladan Allah ne kawai da su.

·Haka ma lallai Allah mai rahama ne ga mutum sama da rahamar da uwa take yi wa xanta, kuma rahamarsa ta yalwaci dukkan komai, don haka wajibi ne a kan bawa ya roqe shi, ya







kuma qasqantar da kansa a gabansa wajen neman buqatunsa na duniya da na lahira, ka da ya roqi kowa.

·Saboda babu wata fa'ida a roqon wani ba Allah ba, babu wanda ke mallakan cikakken iko ban da Allah, babu wanda yake jin abin da ke faruwa a sirri da wajen ganawa in ba Allah ba, babu wanda ke mallakar qaddara wani abu in ba Allah ba, don haka babu mai ikon amsa addu'arsa in ba Allah ba.

·Saboda haka bai halatta ga musulmi ya roqi qabari ba, ko ya roqi na cikin qabarin, ko wane ne aka rufe a cikin qabarin kuwa, saboda ba ya jinsa, ta ma yaya

zai amsa masa ko ya amfane shi? Lallai Allah shi kaxai shi ne mai amfa-

narwa, mai kuma cutarwa, saboda haka bai halatta musulmi ya gina mas-allaci akan qabari ba, domin Annabi (sallallahu alaihi wa sallam) ya hana yin haka.

·Saboda haka wajibi ne akan bawa ya yi duba zuwa ga rauninsa da kuma qarfin Allah mabuwayin sarki, ya kuma sake duba talaucinsa da wadatar Allah maxaukakin sarki, ya kuma duba jahilcinsa da sanin Allah maxau-kakin sarki, ya kuma yin duba zuwa ga qasqancinsa da girman Allah maxau-kakin sarki.

·Ya kuma san cewa lallai girma da buwaya suna ga Allah ne da manzonsa da muminai.

·Domin haka ya wajaba ya zama cikin







waxannan muminan, waxanda ba sa dogara da kowa sai Allah, ba sa neman taimakon kowa sai Allah, ba sa neman tsari daga kowa sai Allah, ba sa neman ceton kowa sai Allah, ba sa tsoron kowa sai Allah, ba sa fatan komai daga wurin kowa sai Allah, ba sa roqon kowa sai Allah, ba sa yanka saboda kowa sai Allah, ba sa bakance saboda kowa sai Allah, ba sa ranstuwa da kowa sai Allah, ba sa xaura layu da tsumburkai, ba sa gasgata bokaye da masu tsubbu da taurari da matsafa, ba kuma sa zuwa wajensu.

·Su ba sa shu'umanci, suna kuma taka-tsantsan da kura-kuren harsunansu kan ka da su ja su zuwa wuta. Ba sa cewa: "Abin da Allah ya so da abin da wane ya so" ko "ba domin Allah da kai

ba" ko "na dogara da Allah da kai", a'a su ne masu cewa: "Na dogara ga Allah shi kaxai" ko " abin da Alah ya so sannan wane ya so"; saboda waxancan kalmomi suna daidaita tsakanin Allah da bayinsa, suna kuma cikin qaramin shirka.

·Kamar yadda ya wajaba mu yi imani da Allah, haka ma ya wajaba mu kafirce wa xagutai.

·Babban xagutu shi ne shaixan, da kuma duk wanda aka bauta masa ba Allah ba da yardarsa.

·A cikin waxanan xagutan akwai wanda duk ya sanya wata doka da ta haramta abin da Allah ya halatta, ko ta halatta abin da Allah ya haramta.

·Haka ma xagutu ne duk wanda ya yi





kira zuwa ga aikata haka, ko ya umurci mutane da shi, ko ya yi hukunci da shi, saboda ya qetare iyakar halitta na ya ji ya kuma bi.

·Allah shi kaxai shi ne ya halicci mutane, ya kuma san mene ne zai gyara su, don haka babu wani wanda ya isa ya sanya masu doka in ba shi ba.

# (2) IMANI DA MALA'IKU

·Na yi imani da mala'ikun da Allah ya halicce su daga haske, ya kuma sanya musu fukafukai, wasu bibbiyu wasu uku-uku wasu kuma hurhuxu. Su kuma ba sa cin abinci, ba sa shan ruwa, ba sa barci, ba sa kuma auratayya, ya umurce su da wasu ayyuka suna kuma aikatawa.

·Mala'iku dawwama suke yi cikin aikin xa'a ba sa gajiya, ba sa kuma savon Allah, suna jin tsoron ubangijinsu da yake sama da su, a cikinsu akwai wanda yake sujada tun ranar da Allah ya halicci sammai da qassai har zuwa ranar alqiyama, idan kuma ya xaga kansa sai ya ce: mun ambaci tsarkinka ya Allah, ba mu bauta maka da bautar





da ta dace da kai ba.

·Su bayin Allah ne, ba kuma mata ba ne, ba kuma mataimakansa ba ne, suna ceton muminai da izinin Allah a ranar alqiyama.

·A cikinsu akwai masu kiyayewa: su ne waxanda suke bai wa bayi kariya ga barin abubuwan qi.

·A cikinsu akwai masu girma kuma marubuta: su ne waxanda suke rubuta ayyukan bayi na alhairi da na sharri (masu kyau da munana)

·A cikinsu kuma akwai masu tasbihi: su ne waxanda suke tasbihi dare da rana ba sa gajiya har zuwa ranar alqiyama.

·A cikinsu akwai masu shawagi: su ne

waxanda suke halartar majalisun zikiri da na karatun Alqur'ani da majalisu na ilimi.

·A cikinsu akwai waxanda suke xaukan al'arshin mai rahama: su takwas ne, su manyan halittu ne daga cikin halittun Allah, tsuntsu zai iya tashi daga gefen kunnen xaya daga cikinsu ya yi tafiyar shekaru xari biyar kafin ya isa zuwa wuyarsa.

·A cikinsu akwai mala'ikan mutuwa: shi ne mai amsar rayukan bayi da izinin Allah, yana da mataimaka.

·A cikinsu akwai Israfilu: wanda zai busa qaho dukkan halittu su mutu kafin tashin alqiyama, sannan ya sake





NI MUSULMI NE

busawa nan take ka gansu a tsaye suna duban juna suna sauraro.

·A cikinsu akwai Mika'ilu: shi ne wanda aka wakkala masa ruwan sama.

·A cikinsu akwai Ridwan: shi ne mai tsaron aljanna, yana da mataimaka waxanda duka suke kai-komo wajen jin daxi da walwalar muminai a aljanna.

·A cikinsu akwai Maliku: shi ne mai tsaron wuta, yana da mataimaka – shugabanninsu su goma sha tara ne- akwai gudumomin qarfe tare da su, suna yi ma kafirai azaba da su ne a cikin wuta,- Allah ya kiyaye mu-.

## NI MUSULMI NE

·Babban mala'iku shi ne Jibrilu: wanda aka wakkala masa wahayi zuwa ga annbawa da manzanni.

·Tabbas Annabi (sallallahu alaihi wa sallam) ya ganshi a sifarsa da Allah ya halicce shi, ya toshe sasanni saboda girmansa, yana fukakai xari shida, shi ne wanda ya kifar da alqaryar Annabi Luxu da gefen fuffukensa, ya xaga ta sama ya juya ta ya kuma kifar da ita, ya sanya samanta ya koma qasa (juyin waina).

·Akwai kuma adadi masu yawa waxanda ba waxannan ba, -babu wanda ya san iyakan rundunar ubangijinka in ba shi ba.





## NI MUSULMI NE

﴿وَمَا يَعْلَمُ جُنُودَ رَبِّكَ إِلَّا هُوَ﴾ [المدثر:٣١]

· Mala'iku suna son muminai waxanda Allah yake sonsu, suna masu addu'a, suna kuma neman masu gafara.

·Mala'iku duk da qarfinsu suna zuwa yaqi tare da muminai.

# (3) IMANI DA LITATTAFAI

·Na yi imani da litattafan Allah waxanda ya saukar zuwa ga manzanninsa, kuma lallai duka –a asalin yadda aka saukar da su- maganar Allah ne da ya yi masu wahayi domin su isar da shari'arsa da addininsa, manyan waxannan litattafai su ne:

·Alqur'ani mai girma da aka saukar wa manzonmu Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam).

·Injila da aka saukar wa Annabi Isah (alaihis-salam).

·At-taura da aka saukar wa Annabi Musa (alaihis-salam).

·Zabura da aka saukar wa Annabi





Dauda (alaihis-salam).

·Da kuma shafukan da aka saukar wa Annabi Ibrahim (alaihis-salam)

·A cikinsu akwai waxanda aka caccanja su kafin saukar da Alqur'ani.

·Kuma lallai Alqur'ani mai girma ya mamaye dukkan waxannan litattafan, shi ne alqali akan dokokinsu da hukunce-hukuncensu, wanda kuma daga saukansa ya share duk wani hukunci na su da ya sava masa.

·Kuma lallai Allah ba zai karvi aiki da komai ba a ranar alqiyama sai aiki da Alqur'ani, ba zai karvi aiki da litattafan da suka gabata ba bayan saukar Alqur'ani ga Annabi Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam).

·Tabbas Alqur'ani magana ne na Allah

mai gajiyarwa, yana da tsarki, varna ba ta zuwa masa ta ko'ina, duk wanda ya yi magana da shi ya yi gaskiya, duk wanda ya yi hukunci da shi ya yi adalci, duk wanda ya yi aiki da shi to kuwa lallai an shiryatar da shi zuwa ga kyakkyawar hanya, duk wanda ya yi riqo da shi ya sami babban rabo kuma ya tsira, wanda kuma ya juya masa baya ya tsinci kansa cikin halakakku.

·Ma'abota Alqur'ani su ne jama'ar Allah kevavvun Allah, fiyayyen mutane shi ne wanda ya koyi karanta Alqur'ani da aiki da shi ya kuma koyar da shi, domin zai zo ranar alqiyama ya yi ceto ga waxanda suka karanta shi suka kuma kiyaye shi sannan suka yi aiki da shi, yana mai neman aljanna ga iyalansa.





·Alqur'ani yana tsarkake zukata ga barin abin da ke gurvata su na abubuwa masu rikitarwa da sha'awaice-sha'awaice, yana kuma kusanta su zuwa ga mahaliccinsu mai girma da xaukaka, yana kuma kwaxaitar da su zuwa ga yin aikin da zasu sami rabo da dawwamammiyar ni'ima.

·Cikin ladubban karanta Alqur'ani akwai:

- Tsarki da alola.
- Fuskantar alqibla.
- Zama cikin ladabi da natsuwa.
- Rashin gaggawa wajen karanta shi.
- Tsoron Allah da qasqantar da

kai.

- Bayyanar da baqin ciki akan zunubai da wuce gona da iri.
- Kuka saboda tsoron Allah da ganin girman maganarsa.
- Rashin xaga murya wajen karanta shi saboda ka da ya daburta masu sallah.
- Lura da tadabburi wajen karanta shi.
- Halarto da zuciya.
- Tunani cikin ayoyin Allah.
- Kuma mu tabbatar da cewa tsayar da hukunce-hukuncen wannan littafin tsakanin mutane shi ne babban dalilin samun xaukaka da nasara akan abokan







gaba a bayan qasa.

Ya xan uwa musulmi ka yi gaggawa zuwa ga ubangijinka, ka riqe wannan littafi gam, ka yi fatar ka da wani ya riga ka zuwa wajen Allah, Allah yana farin ciki da komowarka zuwa gare shi fiye da farin cikin da iyalai suke yi idan wanda ba ya nan a cikinsu ya komo.

# (4) IMANI DA MANZANNI.

·Na yi imani da manzannin Allah, lallai Allah ya zavi manzanni daga cikin mutane, ya yi masu wahayin shari'arsa, ya kuma umurce su da su isar zuwa ga mutane, kuma duk wanda ya bi su zai shiga aljanna, wanda kuma ya sava masu zai shiga wuta.

·Sannan ya qarfafi gwiwarsu da mu'ujuzozi waxanda suka bayyanar da gaskiyarsu, domin su yi amfani da su ga duk wani wanda ya qaryata su, su kuma zama hujja ne a gare su.

·Kuma tabbas farkon manzanni shi ne Annabi Nuhu (alaihis-salam), cikamakonsu kuma shi ne Annabi Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam).





·Kuma mutane ne su, suna cin abinci. Suna sha, suna kuma auratayya, suna rashin lafiya, suna mutuwa, kuma su ne fiyayyun halittun Allah, an katange su ga barin yin savo.

·Manzannin Allah suna da yawa, a cikinsu akwai waxanda Allah ya ambace su a cikin Alqur'ani, waxanda su ne: Annabi Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam) da Ibrahim Khalilur-rahman da Musa Kalimul-lah da Isah Kalmar Allah da Nuhu (alaihimus-salam) waxanda su ne "ulul-azmi" daga cikin manzani (tsira da aminci su tabbata a gare su). Akwai kuma Isma'il da Ishaq da Ya'akub da Haruna da Ayuba da Yunusa da Sulaiman da Dauda da Yahya da Zakariyya da Hudu da Salihu da

Yusuf da Shu'aibu da Ilyasu da Luxu da Zulkifli da Idris da sauransu masu yawa, a cikinsu akwai waxanda Allah ya bayar da labarinsu a cikin Alqur'ani, akwai kuma waxanda bai bayar da labaransu ba.

·Farkon abin da manzanni suka yi kira akai shi ne kaxaita Allah, kuma mafi girman abin da suka hana shi ne haxa Allah da wani a wajen bauta, dukkansu sun zo da musulunci ne da kira zuwa ga kaxaita Allah, duk kuwa da cewa shari'o'insu da hanyoyin yin bautarsu ga Allah mai girma da xaukaka ya xan canja saboda canjin zamunnansu da garuruwansu.

·Kuma lallai manzanni sun yi bishara da zuwan Annabi Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam), sun kuma







umurci mabiyansu da su yi imani da shi (sallallahu alaihi wa sallam) idan an aiko shi suna nan.

·Bambancin dake tsakanin manzo da annabi shi ne: shi manzo an aiko shi ne da sabuwar shari'a, an kuma umurce shi da ya isar da ita zuwa ga mutane. Shi kuwa annabi an aiko shi ne domin ya tabbatar da shari'ar manzannin da suka gabace shi.

·Na yi imani da cewa fiyayyen manzanni a wurin Allah shi ne Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam), shi xin xaya ne daga cikin 'ya'yan Isma'il xan Ibrahim (alaihimas-salam), Allah ya aiko shi zuwa ga mutane baki xaya, da annabcinsa Allah ya cika annabta, da manzancinsa ne kuma Allah ya cika saqwanni.

·Ya qarfafe shi da mu'ujuzozi, ya kuma fifita shi akan dukkan manza-nninsa kamar yadda ya fifita saqonsa akan dukkan saqwanni, ya kuma xaukaka shari'arsa akan dukka shari'o'i, littafinsa ma –Alqur'ani- ya fifita shi akan dukkan litattafai, al'um-marsa ma –musulmai- ya fifita su akan saura al'ummatai.

·Ubangijinsa ya ba shi abin da bai baiwa wani annabi kafinsa ba, a cikin abubuwan da ya ba shi akwai:

1) Alwasilat: ita ce babban matsayi a cikin aljanna, Allah ya tanadi wannan matsayi ne domin Annabi (sallallahu alaihi wa sallam)
2) Alkausar: wani kogi ne a cikin







aljanna, yana gudana ne ta qarqashin al'arshi.

3) Alhaudhu: shi ne tafkin ruwan da babu wanda zai sha shi a ranar alqiya sai musulmi.

ranar da mutane zasu sha matsanancin qishin ruwa, gumi ya mamaye jikkunansu tun daga gwiwowinsu har zuwa cikkunansu da kafaxunsu, kowa gwargwadon abin da ya aikata, musulmai zasu sha wannan ruwan ne da kofunan da Annabi (sallallahu alaihi wa sallam) zai ba su da hanna-yensa masu girma da albarka, bayan haka ba zasu qara jin qishirwa ba har abada.

4) Ceto: wannan shi ne matsayin da ake cewa da shi "maqamul-

mahmud" a ranar alqiyama; lallai manzon Allah (sallallahu alaihi wa sallam) zai yi ceto a wurin Allah, har ya fitar da musulmai masu laifi daga wuta, ta yadda babu wani da yake faxin "La'ilaha illallahu Muhammad ur-rasulullahi" da zai yi saura a cikinta, mai savo ba zai dawwama cikin wuta ba, za a fitar da shi bayan an tsarkake shi daga savonsa.

·Duk wanda ya yi imani da dukkan annabawa amma bai yi imani da Annabi Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam) ba, to kuwa lallai ba zai tava fita daga wuta ba.

5) Kuma lallai Allah ya taimake shi, ya kuma taimaki rundunarsa da





mabiyansa har zuwa ranar alqiyama, ta hanyar saka tsoro da razana a zukatan maqiyansu na tsawon tafiyar wata, ba a kuma bayar da haka ga wani annabi kafinsa ba (sallallahu alaihi wa sallam).

6) An sanya qasa a gare shi da sauran musulmai ta zamo wajen sujada, kuma mai tsarki, wannan ma ba a bai wa annabawan da suka gabace shi ba.

7) Allah ya aike shi zuwa ga mutane da aljannu baki xaya, sa'ilin da ya aiki kowane Annabi zuwa ga jama'arsa kaxai.

8) Kuma lallai shi ne farkon wanda qabarinsa zai tsage ya fito, farkon

mai ceto, kuma farkon wanda zai qwanqwasa qofar aljanna, sai Ridwan –mai tsaron

aljanna- ya ce: wane ne? sai ya ce: Muhammadu ne, sai Ridwan ya ce: kai kaxai aka umurce ni da na buve wa, ka da kuma in buxe wa wani kafinka.

A cikin mu'ujuzozinsa (sallallahu alaihi wa sallam) akwai:

- Tsagewar wata.
- Ya mayar wa Qatadatu idonsa da aka cire masa a ranar Uhdu, wannan idon kuma ya zamo ya fi lafiya akan xayan.
- Ya mayar da maqyangyamar Ibnul-Hakam lokacin da aka karya ta a ranar Badar.







- Ya nemi bishiya da ta yi shaida, kuma ta shaida da "shahad-ataini" har sau uku a gaban wani kafiri, ya kuma musulunta.
- Kukan kututturen bishiya wanda manzon Allah (sallallahu alaihi wa sallam) yake huxuba a kansa lokacin da ya bar shi, bai kuma yi shiru ba sai da (sallallahu alaihi wa sallam)ya xaura hannayensa a kanshi.
- Haka ma yawaitar abinci a hannunsa (sallallahu alaihi wa sallam) har mutane sama da tamanin suka ci gwargwadon tafuka biyu na abinci suka kuma qoshi.
- Haka ma yawaitan ruwa a ranar

Hudaibiyya, lokacin da ruwa ya qare wa runduna ba su da sama da kimanin kofi xaya, sai Annabi (sallallahu alaihi wa sallam) ya sanya hannunsa, nan take sai ruwa ya ci gaba da vuvvugowa daga yatsunsa masu albarka (sallallahu alaihi wa sallam), mutane suka sha suka kuma yi alola, kuma adadinsu ya kai kimanin mutum dubu xaya da xari huxu.

- Haka ma an yi tafiya da shi zuwa "Masjidu- al-aqsa", sannan an yi "Mi'iraji" da shi zuwa maxau-kakan sammai har zuwa magar-yar tuqewa.
- A cikin mu'ujuzozinsa (sallallahu alaihi wa sallam) akwai labarai





na al'ummatan da suka gabata da na annabawansu,

tabbas shi "ummiyyi' ne, ba ya karatu balle rubutu. Haka ma bayar da labarin abin da zai faru nan gaba na buxe Parisa da Rum, da kuma kekketa mulkin Kisra da ya keta saqon manzon Allah (sallallahu alaihi wa sallam), da ma wasunsu na mu'ujuzozi masu yawa.

- Mafi girman mu'ujuzarsa shi ne Alqur'ani mai girma, shi ne kuma dawwamammen mu'ujiza har zuwa ranar sakamako.
- Sannan Allah ya xaukaka amba-tonsa (sallallahu alaihi wa sallam) ta yadda mai girma da xaukaka ya gwama sunansa da sunansa, ya

kuma sa kalmar shahada "La'ilaha illallahu Muhammad ur-rasulullah" ta zamo farkon abin da bawa zai shiga musulunci da ita, kuma qarshen abin da ya kamata bawa ya bar duniya da ita, duk wanda maganarsa ta qarshe ta zama "La'ilaha illallahu" to kuwa ya shiga aljanna.

- Game da Annabinmu (sallallahu alaihi wa sallam) ya zama wajibinmu ne ka da mu gabatar da maganar kowa a cikin halittu akan maganarsa, ko ra'ayin kowane mai bi akan umurninsa, idan wasu mutane sun riga ka yin hijira zuwa gare shi (sallallahu alaihi wa sallam), to kai ma ka yi hijira zuwa ga sunnarsa a cikin





dukkan al'amurranka, ka da ka bi kowa in ba shi ba.

Mu haxa kai gaba xaya akan umurninsa, mu yi masa biyayya

﴿مَّن يُطِعِ ٱلرَّسُولَ فَقَدۡ أَطَاعَ ٱللَّهَۖ﴾ [النساء: ٨٠].

(sallallahu alaihi wa sallam), saboda duk wanda ya yi wa manzo biyayya to kuwa lallai ya bi Allah.

- Ka da mu kira shi ba da manzon Allah (sallallahu alaihi wa sallam) ba, ka da mu ce da shi "Muhammadu" kawai.
- Mu ladabtu da ladubbansa, mu yi koyi da shi a dukkan halayensa (sallallahu alaihi wa sallam) a wurin barcinsa ne ko warin cin abincinsa da tafiyarsa da sallarsa da azuminsa da sadakarsa da

jahadinsa (sallallahu alaihi wa sallam).

- Mu so shi fiye da yadda muke son kanmu da 'ya'yanmu da iyaye-nmu da ma mutane baki xaya.

· Kuma dole ne mu so duk wanda yake son manzon Allah (sallallahu alaihi wa sallam), yake kuma koyi da shi. Mu kuma qi mai qin manzon Allah (sallallahu alaihi wa sallam), yake kuma qin lizimtar shari'arsa.

· Ya zama wajibi akan musulmi ya so muminai, ya kuma taimake su, ya yi kama da su, ya kuma damu da al'amurransu, ya taimake su wajen aikin alhairi, ya riqe su a matsayin abokai.

· Wajibi ne a gare shi ya qi kafirai da





kafircinsu, ka da ya yi masu biyayya, ka da ya haxa kai da su wajen cin mutuncin musulmai, ka da ya taimake su akan varnarsu, ka da ya yi tarayya da su a bukukuwansu, kuma haramun ne ya zalunce su, dole ne ya yi masu adalci.

· Wajibi ne mu so iyayen muminai, matan Annabi (sallallahu alaihi wa sallam), mu kuma so sahabbansa (sallallahu alaihi wa sallam); saboda su ne fiyayyun mutane bayan annabawa.

· Haka ma ya wajaba mu rayar da sunnarsa (sallallahu alaihi wa sallam), mu kuma bayyanar da shari'arsa, mu kuma isar da kiransa zuwa ga mutane baki xaya, sannan mu yi haquri akan abin da zamu gamu da shi na cutarwa game da hakan, hakan dole ne.

·Saboda lallai sunnar Allah za ta ci gaba da gudana akan halittunsa, saboda babu wani annabi daga cikin annabawa ko waliyyi da ya yi kira zuwa gaskiya face an qi shi kuma an cutar da shi.

·ya kai musulmi, ka faxaka, ka da ka yarda cutarwar da kafirai suke maka ta kawar da kai ga barin addininka, domin an cutar da manzon Allah (sallallahu alaihi wa sallam) lokacin da yake cikin sahabbansa marasa yawa, an kuma cutar da sahabbansa sun yi haquri.

·Ka da wai danganta ka da rashin hankali da rashin tunani da ci baya su sa himmarka ta yi rauni, ko su ce: an







yi maka wankin qwaqwalwa. Kyakky-awar koyi da manzon Allah ya wajaba a gare ka, domin dai tabbas wasu sun ce da shi: mawaqi wasu kuma sun ce: mahaukaci.

·Ka da ka damu idan an ce maka: mai tsattsaurar ra'ayi ko vatacce. Wannan shi ne halin kafirai tare da muminai:

﴿وَإِذَا رَأَوْهُمْ قَالُوٓاْ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ لَضَآلُّونَ﴾ [ المطففين: ٣٢].

(idan sun gansu sai su ce: lallai waxannan tabbas vatattu ne) [32, mutaffifina]

·Shin bai ishe ka ba idan aka ce mutane sun kasu kashi biyu kai ka zamanto a cikin kashin da Annabi (sallallahu alaihi wa sallam) yake?!

· ﴿ يَوْمَ يَعَضُّ ٱلظَّالِمُ عَلَىٰ يَدَيْهِ يَقُولُ يَٰلَيْتَنِى ٱتَّخَذْتُ مَعَ ٱلرَّسُولِ سَبِيلًا ﴾ [الفرقان:٢٧].

**Ka qyale su har zuwa ranar da azzalumi zai ciji yatsarsa yana mai cewa: kaico na, ina ma na bi hanya tare da manzon Allah.**

**·Ka da ka ruxe idan sun ce maka xan ta'adda, ko asharari, wannan qarerayi ne na azzalumai a kan muminai duniya da lahira, domin lokacin da mika'ilu suka kora su akan fuskokinsu zuwa jahannama, suka yi ta duba cikin suka ce:**

﴿وَقَالُوا۟ مَا لَنَا لَا نَرَىٰ رِجَالًا كُنَّا نَعُدُّهُم مِّنَ ٱلْأَشْرَارِ ﴾ [ ص:٦٢].

**mene ne ya sa ba mu ganin mutanen da muka qirga su cikin ashararai?**







**·A nan ne muminai zasu kira su (waxanda suka kira su da ashararai) daga babban matsayi a cikin Firdausi, su ce:**

﴿أَن قَدْ وَجَدْنَا مَا وَعَدَنَا رَبُّنَا حَقًّا﴾ [الأعراف:٤٤].

**(Lallai kan mu mun sami abin da ubangijinmu ya yi mana alqawari gaskiya ne) [44, al-a'arafi]**

# (5) IMANI DA RANAR LAHIRA

· Na yi imani da ranar lahira, ita ce ranar da duniya za ta qare (gidan aiki), ranar lahira kuma ta fara (gidan sakamako), masu biyayya a saka masu da aljanna, masu savo kuma a saka masu da wuta.

· A ranar alqiyama ne ake sanya mizani, a kuma baiwa kowane bawa littafinsa, duk wanda ya amshi littafinsa da hannun damansa to kuwa lallai yana tare da Annabi (sallallahu alaihi wa sallam) a aljanna, wanda kuma duk ya amshi littafinsa da hannun hagunsa to kuwa lallai yana tare da Fir'auna (Allah ya la'ace shi) a cikin wuta.





· Ana kafa siraxi, duk wanda ya qetare shi ya shiga aljanna, wanda kuma tsininsa ya fizgo shi saboda mugun aikinsa zai faxa wuta.

· Ranar alqiyama tana da alamu manya da qanana.

· A cikin qananan alamun akwai: tozarta amana da yawan kashe-kashe, ka ga fasiqai sun xauki jan ragamar al'umma da qarfi, sannan wawaye su riqa magana akan al'amurran al'umma masu muhimmanci.

· A cikin manyan alamun akwai: bayyanar Mahdi da tsayuwan Hali-fanci na gaskiya akan tsari irin na Annabi kafin tashin alqiyama da fitowar Dujal.

· Da saukowar Annabi Isah (alaihis-

salam) domin ya jagoranci musulmai ya kuma yaqi kafirai,

ya kuma karya kuros, ya kashe alade, ba zai yarda da komai ba sai musulunci.

· Babu wani gida -a birni ko a qauye- da zai saura face Allah ya shigar da wanan addinin ko dai girman mai girma ko da qasqancin qasqantacce.

· Da fitowar Yajuju da Majuju, haka ma fitowar dabbar da za ta yi magana da mutane, da hudowar rana daga mafaxarta da xauke Alqur'ani da makamantan haka.

· Duk wanda ya aikata wani aiki na alhairi ko sharri ko da gwargwadon qwayar zarra ne zai gani a ranar alqiyama a cikin littafinsa.







· Ku yi gaggawa zuwa ga aikata ayyukan xa'a tun lokacin rubuta su bai qare da mutuwar bawa ba, a kuma lokacin da babu wanda ya sani sai Allah.

· Iyalinsa su yi masa wanka, su kuma yi masa likkafani, su yi masa sallah su binne shi, mala'iku biyu su zo masa "Munkar" da "Nakir" su zaunar da shi su tambaye shi: wane ne ubangijinka? Mene ne addininka? Wane ne annabinka?

· Idan ya amsa da cewa: Allah shi ne ubangijina, kuma Musulunci shi ne addinina, Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam) shi ne annabina kuma manzona – Allah ya katartar da shi zuwa ga haka- za a buxe masa taga cikin qabarinsa har ya zuwa aljanna,

ya hango mazauninsa a can, da benensa da mulkinsa, ya kama farin ciki, a kuma yalwata masa qabarinsa iya ganinsa.

· Idan kuma yana cikin kafirai ne, to ba zai iya amsawa da komai ba, amsa a wannan lokacin ba wai wayau da kaifin qwaqwalwa ke kawo ta ba.

Sai dai Allah yana tabbatar da ma'abota imani a wannan lokaci; saboda abubuwan da suka gabatar na kyawawan ayyuka da kaxaita Allah, da bayar da farillai da jahadi da biyayya da umurni da aikin alhairi da hana munanan ayyuka da sadaka da karatun Alqur'ani da azumi a lokacin garji da tsayuwar darare masu tsawo da sanyi.







· Amma idan ya zamo kafiri ne shi, to lallai qabarinsa zai quntata har kafa-xunsa su shige cikin jikinsa, qabarin na sa ya zamo rami ne daga cikin ramu-kan wuta saboda mum-munar aikinsa.

· Ya xan uwa musulmi, ka yi qoqari, yanzu lokaci ne na aiki ba hisabi, gobe kuma ranar hisabi ne babu aiki.

· A wannan rana ce musulmai masu biyayya -su kaxai- zasu shiga aljanna, saboda Allah ba zai karvi komai ba a ranar alqiyama sai musulunci.

· A cikin aljanna akwai ni'imar da kunne bai tava ji ba, ido bai tava gani ba, kuma ba ta tava xarsanuwa a cikin zuciyar wani mutum ba. Kuma ni'imarta za ta dawwama har abada ba yankewa, mutanen cikinta ba zasu

mutu ba, mafi girmar ni'ima ita ce duba zuwa ga zatin Ubangijin talikai.

·Masu savo da fajirai da kafirai zasu shiga wuta, a cikin wuta akwai azaba mai tsanani, wadda Allah ya tanadar wa kafirai, manyan duwatsu kafaffu ma ba zasu iya jurewa ba, a can ne za a yi ta azabtar da su babu qaqqautawa.

· A can ne mabiya xagutai zasu yi addu'ar a ruvanya azaba

ga shugabannin da suka vatar da su, sai Allah ya bayar da umurnin a ruvanya azaba a gare su baki xaya.

· Ya xan uwana musulmi ka dawwama akan gaskiya, ka da yawan waxanda suka sava ya ruxe ka, saboda idan har ka bi mafi yawan waxanda suke a bayan qasa zasu vatar da kai ga barin





NI MUSULMI NE

hanyar Allah, kai dai ka ci gaba ta tafiya tare da masu zuwa wajen Allah.

· Domin dai tabbas samun wasu jama'a masu riqo da gaskiya a cikin al'ummar Annabi Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallam) abu ne wanda ba zai gushe ba, wanda ya sava masu ko ya bayar da su ba zai rage su da komai ba har zuwa tashin alqiyama.

· Shin ina dubara ta riskar waxannan darajoji da tsira, da kuma nesantar waxancan azabu? Ina dubara ta cin ma waxancan magabata makusanta da kuma nesantar waxancan masu juya baya kuma halakakku? Lallai babu wata hanya sai tuba ta gaskiya da za ta gyara abin da ya wuce, da kuma aiki na gari da zai gyara abin da ya yi saura na rayuwa, da kuma kyakk-

yawar xammara wajen tsayawa daidai akan hanya babu karkata.

· Ka zamo kana tare da mutane da jikinka, ka siya ka siyar ka yi aure, ka raya duniya da abin da Allah ya halatta maka.

· Ka da ka xamfara komai na duniya da zuciyarka, ka tafi da zuciyarka zuwa in da ya kamata ta kasance, can qarqashin al'arshin mai rahama, ka yi sujada da zuciyarka, sujadar da babu xagowa har zuwa ranar tashin alqiyama.





# (6) IMANI DA QADDARA

· Shi ne mu yi imani da cewa lallai Allah ya san duk abin da yake a cikin wannan duniya, haka ma duk abin da ya kasance da wanda zai kasance a gaba har zuwa ranar alqiyama, kai daidai da sanin halin qwayar zarra bai kuvuce masa ba.

Kuma lallai tabbas ya san ayyukan bayi da arzikinsu da lokutan ajalinsu, kuma su wane ne 'yan aljanna a cikinsu, su kuma wane ne 'yan wuta tun kafin ya halicce su.

· Kuma lallai Allah ya rubuta waxannan qaddarorin a cikin "Lauhul-mahfuz" tun kafin ya halicci sammai da qassai da shekaru dubu hamsin, kuma wannan "Lauhul-mahfuz" xin

babu wanda ke leqa shi, shin shi mala'ika ne makusanci ko kuwa annabi mursali.

· Kai har jinjiri a cikin mahaifiyarsa Allah zai umurci mala'iku da su rubuta shi a matsayin namiji ko tamace, su kuma rubuta arzikinsa da aikinsa da ajalinsa da makomarsa (zuwa aljanna ko wuta), su kuma rubuta abubuwan da zasu faru da shi na alhairi ko na sharri.

· Sannan a daren "Lailatul-qadri" abubuwan da aka qaddara zasu faru a shekara su sauka daga "Lauhul-mahfuz", na ajalin mutane ne da arzikinsu da wanda zai yi aikin hajji a cikin wannan shekarar da dai makam-antan haka, a dai qaddara duk abin da zai faru a cikinta a wannan daren.





· Sannan abubuwan da aka qaddara su faru kullum a lokutansu a kuma kan abubuwan da aka qaddara masu haka, Allah ya xaukaka wasu mutane, ya kuma qasqantar da wasu.

· Mun yi imani da cewa duk abin da Allah ya so shi ne zai faru, abin da ya so ya faru, abin da bai

so ba ba zai faru ba, babu wanda ya isa ya rinjayi Allah, kuma lallai shi ne ke juya zukata, yana shiryatar da wanda yake so da falalarsa da rahamarsa, ya kuma vatar da wanda ya so da adalcinsa da hikimarsa, shi xin ya san wanda ya cancanci shiriya kamar yadda ya san wanda ya cancanci vata.

· Shi Allah ba a tambayarsa akan abubuwan da yake aikatawa, mutane

ne kawai ake tambayarsu.

· Kuma lallai mun yi imanin cewa Allah shi ne ya halicci dukkan komai, babu daidai da qwayar zarra a wannan duniya face Allah shi ne ya halicce ta, ya kuma halicci motsinta da shirunta.

· Kuma lallai ya halicci bayi da ayyukansu, shi kuma ya halicci iko da qudura ga bayi domin su zavi ayyukansu da kansu.

· Kuma lallai Allah maxaukakin sarki ya umurci halittunsa su yi masa biyayya, ya kuma yi masu alqawarin aljannarsa, ya kuma hana su aikata savo, ya kuma yi wa masu savo gargaxi da wutarsa, bai wajabta masu wani aiki ba sai abin da zasu iya, daga nan sai





suka kasu kashi biyu: Muminai da Kafirai, su suka so haka suka kuma zava, duk hakan Allah ne ya halitta masu ikon yin hakan a cikinsu.

· Kuma lallai lada da azaba suna zuwa ne gwargwadon yadda mutum yake wajen bin shari'a, ba wai akan sanin da ya yi masu tun asali ba, duk wani wanda ya yi aiki ko da gwargwadon qwayar zarra ne na alhairi zai sami lada, haka ma wanda ya yi wani aiki ko da gwargwadon qwayar zarra ne na sharri za a yi masa uquba akan haka.

·Kuma lallai abin lura shi ne qarshen ayyuka, kuma kowane bawa an sawwaqe masa abin da aka

halitta dominsa na jin daxi a aljanna ko shan wahala a cikin wuta.

**·Saboda haka ne ya zama dole bawa ya ji tsoron mummunar makoma, ya dage wajen roqon Allah, yana mai nuna talaucinsa zuwa gare shi kan ya shiryatar da shi zuwa ga hanya madaidaiciya, ya kuma dawwama wajen neman taimakonsa a kan yin masa xa'a, ya kuma ci gaba da neman tsarin kar ya sava masa; saboda bawa ba shi da wani iko akan duka waxannan halaye in ba da qaddarawar Allah ba.**

**·Kuma tabbas muminai sun yarda da qaddarar Allah da ikonsa na alhairi da sharri a cikin abubuwa masu xaci da masu daxi, kuma suna da yaqinin cewa babu wani da ya isa ya amfane su sai idan Allah ne ya qaddara, kamar yadda babu wanda zai cutar da su sai da abin da Allah ya rubuta.**







**·Babu yadda za a yi bawa ya sami garxin imani sai idan ya san cewa: duk abin da ya same shi dama ba zai tava kuskure masa ba, abin da kuma ya kuskure masa ba zai tava samunsa ba.**

**·A qarshe: ina gode wa Allah, ina kuma roqonsa kan ya shigar da ni aljanna, ni da sauran musulmai, ya kuma kare ni ga barin wuta, ni da sauran musulmai, amin.**

***ALLAH KA YI SALATI GA ANNABI MUHAMMADU DA ALAYENSA DA SAHABBANSA KA KUMA YI TSIRA A GARE SU.***

***QARSHEN ADDU'ARMU SHI NE: (GODIYA TA TABBATA GA ALLAH UBANGIJIN TALIKAI).***